# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Almara a Afirka domin al'adu da zaman lafiya:
## Bari na ba ku labari
## Na tara: Wanda ya fi kowa kyau


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Ibrahima Ndiaye |
| Waɗanda suka tace: | Yann Durand, Stefanie Duckstein, Naïma Guira |
| Wanda ya fassara: | Ɗanlami Bala Gwammaja |


**'Yan wasa:**

Mai ba da labari

Ɗawisu

Wakili

Aku

MAI GABATARWA:

Masu sauraronmu, barkanmu da sake saduwa da ku a shirinmu na “Ji Ka Karu” kashi na tara mai taken “Bari na ba ku labari”, mai bayani a kan hikayoyi masu koya zamantakewa tsakanin al’umma. A yau za mu yi dogon waiwaye ne cikin zamanin da ya shuɗe. A wannan kashin za mu ji dalilin da ya sa jiji da kai ba shi da kyau, da kuma yadda aka yi wa dawisu horo saboda jiji da kai. Ku ba mu aron kunnuwanku ku saurari shirin mai suna: “Wanda ya fi kowa kyau”.

MAI BA DA LABARI:

Shekaru aru-aru da suka wuce, zamanin da aka fara amfani da lokaci, Juhurma wanda shi ne ya halicci dabbobi sai ya samar da halittu masu fikafikai don su rayu a doron ƙasa. A nan ne ake ganin tsuntsaye za su hayayyafa su kuma rayu cikin kwanciyar hankali. A wannan zamanin Kaza tana da haƙora, kuma Ɗawisu fari ne sal kamar gishiri. Waɗannan tsuntsaye sun zauna da juna a doron ƙasa lafiya kuma cikin jin daɗi. Akwai wadataccen abinci da kuma isasshen ruwa da kowa ke buƙata. Sai dai bayan saukarsu a doron ƙasar, Wakilin da Juhurma ya naɗa a matsayin Sarki sai ya yi wannan jawabin:

WAKILI:

“Ya ku ’yan’uwana maza da mata, ba shakka akwai wani dalili da ya sa aka samar da mu a doron ƙasa. A karon farko, an ƙyale mu mu nema wa kanmu makoma. Allah ne kaɗai ya san me zai samu nan gaba. Amma duk da haka, abin da muka shuka, to ku tabbata shi za mu girba. Ya rage namu mu tashi tsaye mu san yadda za mu zauna da junanmu lafiya, kuma cikin farin ciki. Ina yi muku fatan alheri.”

MAI BA DA LABARI:

Sarki yana gama wannan jawabi sai ya sallami kowa. Don haka, kowa na iya tafiya ya ci gaba da harkokinsa ya kuma shaƙata gwargwadon

hali da buƙatunsa. Kome lafiya lafiya, kuma tsuntsaye suna rayuwa ne cikin yanayi mai daɗi.
Wata rana kwatsam, sai wani hunturun sanyi ya haike wa wannan daula tasu. Wannan hunturu ya cutar da tsuntsaye ƙwarai da gaske. Shi Ɗawisu wanda yake da gashi mara yawa ya fi kowa galabaita, don da da ma gashin nasa ba a yi shi ne don ya jure irin wannan yanayi ba. Ba shakka ya kaɗu kamar kazar da ruwa ya daka.
Tari fa ya kama Ɗawisu ba ƙaƙƙautawa, ga kuma zazzaɓi. Don ya samu kuɓuta daga wannan hali da ya samu kansa a ciki, sai ya je wajen Wakili, wato sarki, ko ya sami mafita, da kuma shawarwari.

ƊAWISU:

"Ka ji ƙaina, ranka ya daɗe, ba zan iya jure wannan yanayi ba! Sanyin nan ya tsananta! Duk borin jini ya fito a jikina sai ka ce wata agwagwar ruwa! In ba ka yi agaji ba, to fa kome na iya faruwa a gare ni, ba kuma nan da daɗewa ba."

MAI BA DA LABARI:

Tausayi ya kama Sarki, sai nan take ya sa masinjansa, wato Aku, ya tara masa jama'arsa. Dukkan tsuntsayen kuwa sai da suka halarta. Saboda ganin yadda Ɗawisu ya gigita, sai duk suka tsaya suka kuma tallafa masa. A bisa umarnin Sarkin, sai kowa ya ba wannan maririn tsuntsu bargo mai ɗumi. Sannan kuma sai duk suka duƙufa a kan Ɗawisun suka lilliƙa masa gashinsu a jikinsa da kwaɓaɓɓen garin kuka. Bayan sun gama, sai kowa ya koma gida. Lokacin da Ɗawisun ya sami sauƙi, sai kuma ya shiga barci.
Bayan 'yan satuttuka sai bazara ta shigo, da wannan yanayin nata mai ƙawata wuri. Sai kuma rana ta ɗumama doron ƙasa da haskenta. Don murnar zagayowar yanayi mai daɗi, wanda aka ƙagu ya dawo, sai Sarki ya yanke shawarar yin gagarumin biki a fadarsa. Kamar yadda aka saba, sai aka umarci Aku ya yi yekuwa ya sanar da kowa da kowa. Don haka, sai ya bi duk jama'ar garin ɗaya bayan ɗaya yana sanar da su da kansa.

AKU:

“Tsarki ya tabbata ga rana! Tsarki ya tabbata ga rana! Sarki yana gayyatar kowa da kowa zuwa shagalin bikin maraba da bazara. Tsarki ya tabbata ga rana! Tsarki ya tabbata ga rana!”

MAI BA DA LABARI:

Har Ɗawisu ma da bai gama wattsakewa daga barci ba ya sami labarin. Washegari kowa ya halarci wannan taro, amma ban da Ɗawisu, don kuwa ya tafi rafi ya salla wanka don ya fito fes. Yana shirin nutsa kansa cikin ruwa ke nan sai ya ga siffarsa, ya kuma lura da wani abin mamaki, wato yadda ya dawo kyakkyawan gaske. Wani irin kyau wanda har yau ɗin nan ana faɗarsa. Gashinsa ya yi sinkif ya kuma yi launi iri dabam-dabam, sai sheƙi yake yi. Har wata toliya ce ma ta tsiro a kansa, wato fitacciyar toliyar nan da aka san shi da ita mai siffar mataji. Saboda da haka sai ya yi wanka a hankali, ya kuma tsaya a tsanake ya sharce gashin nan nasa mai ƙyalƙyali sannan ya baza shi a rana.

Daga ƙarshe, sai Ɗawisu ya garzaya ya nufi wurin taron yana taƙama da wannan sabuwar siffa tasa. A wannan lokacin kuwa ana tsaka da shagali, amon ganguna na tashi, tsuntsaye na busa iri-iri. Da ganin Ɗawisu sai kowa ya yi tsit, saboda ganin irin rikiɗar da wannan makararren ya yi.

AKU:

“Wannan kuwa Ɗawisun namu ne wanda muka sani!?”

MAI MAGANA:

Kai! Amma kuwa da kyan gani yake!

AKU:

“Tsarki ya tabbata ga rana! Tsarki ya tabbata ga rana!”

MAI BA DA LABARI:

Kowa sai faɗin albarkacin bakinsa yake yi a wurin. Abin ya burge dukkan tsuntsayen da suke wurin. Shi kuma Ɗawisu sai wata tafiyar taƙama yake, yana zagayawa kamar wanda yake karɓar faretin ban girma, yana kuma baza gashin nan nasa mai ƙyalƙyali. Da ya zo gaban Sarkin, sai ya ɗan duƙa, ya yi kamar yana ba da haƙuri saboda makara da ya yi, sannan ya juya ya kalli sauran, ba kunya ba tsoron Allah, ya fara jawabi:

ƊAWISU:

“Ina miƙa godiyata a gare ku saboda karamcin da kuka nuna a gare ni! A yanzu, na fi kowa kyau a nan! Daga yau, ina son ku dinga kirana da ‘Santali, Sarkin kyawun wannan daji’!”

MAI BA DA LABARI:

Wannan hali na jiji da kai ya ɓata wa waɗanda suka taimaka masa da barguna lokacin hunturu rai sosai. Wasu daga cikin tsuntsayen tuni sun yanke shawarar cewa za a fiffige gashin ɗawisu duka saboda harzuƙar da suka yi. A lokacin ne Sarki ya sa baki yana daga kan karagarsa, don kada a yi ɓatacciya, ya kuma yi ƙoƙarin yi wa Ɗawisun uzuri:

WAKILI:

“Ɗawisu a gasikya ka yi kyau, amma na banza. Kuma bari ka ji: za ka ga abin da wannan jiji da kan naka zai jawo maka. Je ka, ka gani. Ba abin da zan kuma cewa. A ma tashi daga bikin haka!”

MAI BA DA LABARI:

Washegari da sassafe, sai Allah ya fara bayyana bakan gizo. Sai dukkan tsuntsayen suka ruga don su gane wa idonsu irin wannan tataccen aiki na hikima.
Cikin yanayi na zumuɗi, sai tsuntsayen nan suka dinga tafa fikafikansu, suna cara, suna busa, suna kuma karkaɗa haƙora cikin

farin ciki. A wannan lokacin sai Ɗawisu ya zo, nan take sai kishin adon nan na bakan gizo ya kama shi. Sai ya kama baza jelar nan tasa mai kama da wili, amma ba wanda ma ya san yana yi. Saboda jin an wulaƙanta shi sai ya yi ta kuka har muryarsa ta dashe.

Amma akasin da aka samu shi ne ba wani magani, don haka muryarsa ta dashe ke nan har abada. Tun daga ran nan kuwa, sai ya zamana kyau dai akwai shi a wurin Ɗawisu, amma da zarar ya buɗe baki ya yi magana, sai kowa ya watse, kuma har yanzu, haka abin yake.

Wannan ita ce hikayar tamu, a saurara, a yi amfani da darasin da take koyawa, ko a rabauta.

MAI GABATARWA:

To masu sauraronmu, a yau kuma a nan za mu dasa aya a cikin shirin namu mai taken "Wanda ya fi kowa kyau". Wannan wane irin ƙarkon kifi Ɗawisu ya yi! A ƙarshe ya jawo wa kansa matsala da kansa. Amma anya ba shi ke da laifi ba kuwa? Ba a garin jiji da kansa da son a sani ya sami kansa a wannan halin ba? Ko kuna ganin sauran tsuntsayen sun matsa masa ne kawai? Ku faɗa mana, muna so mu sani! Kuna iya rubuto mana ra'ayoyinku a dangane da wannan shiri ko kuma sake sauraronsa ta adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe.

Ibrahim Ndiaye ya rubuta wannan hikaya.